Sallah a cikin masallacina wannan (ita ce) mafi alheri daga sallah dubu a cikin waninsa sai dai Masallaci mai alfarma

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Sallah a cikin masallacina wannan (ita ce) mafi alheri daga sallah dubu a cikin waninsa sai dai Masallaci mai alfarma".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yana bayyana falalar sallah a masallacinsa, kuma cewa shi yafi yawan lada daga sallah dubu a cikin waninsa daga masallatan duniya, sai dai Masallaci mai alfarma a Makka, shi ne mafifici daga sallah a cikin masallacinsa - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/65090